## Children's Consecration to Our Lady

Mary, my Mother,
today I come to you with joy,
to give you my whole heart.
I give you everything I have
and everything I da,
my whole lif e.
Ta you I bring every single person,
that I hold in Love in my heart:
my parents, my brothers and my sisters,
all my friends,
but also those who have hurt me.
Be a Mother to us all,
bless and protect us.
I wish to be your child,
to Love you as my Mother
and pray faithf ully to you.
Help me to remember, each day,
that I belang to you.
Mother, I am yours, now and f or all eternity.
With you and through you
I want to belang completely to Jesus.

Amen.

# KIMANIN YARA MILIYAN DAYA

## DOMIN ADUÁR ROZARI



Domin hadin kai da salama

ranar 18 ga Oktoba


Aid to the Church in Need
ACN INTERNATIONAL

www.millionkidspraying.org info@millionkidspraying.org

# Rosari Maria

1. Cikin sunan Uba
2. Ina ba da gaskiya
3. Ubanmu
4. Ageishe ki Maria x 3
5. Daukaka ga
6. Ya Yesu
7. Announce the mystery of
   the day then repeat 3.
8. Hail Mary

   x 10 then repeat 5 and 6.
9. Repeat 7 and 8 until you complete the
   whole mysteries of the day.
10. Ageishe ki Sarauniya mai Tsarki

## Cikin sunan Uba

Cikin sunan Uba, da na Da, da na Ruhu mai Tsarki. Amin.

## Ina bada gaskiya ga Allah

Ina bada gaskiya ga Allah, uba madaukaki, mahalicin sama da kasa. ina bada gaskiya ga yesu kristi, dan shi madaukaki, ubangijin mu. Ake dauke cikin shi a wurin ikon Ruhu mai Tsarki, kuma aka haife shit a wurin budurwa Maria. ya sha wahala kalkashin piyus bilatus, aka kasha shi, ya mutu, aka bizne shi. ya sabka ta cikin jahanama. ran kwana na uku ya tashi kuma. ya hau zuwa sama, yana zamne a hannu daman a uba. zaya komo kuma domin ya shari'anta masu rai da matatu. na bada gaskiya da ruhu mai tsarki, da ikiliziyar catolika mai Tsarki, da zumutar tsarkaka, da gafarar zunubai, da tashin matatu da rai har abada. Amin

## Ubanmu

Ubanmu wanda ke cikin samaniya, a tsarkake sunanka, mulkin ka shi zo. abin nufin ka a yi shi a cikin duniya kamar yadda a ke yinsa cikin sama. ka ba mu yau abincin yini, ka garfata mana laifin mu kamar yadda mu ke gafarta ma wadanda su ke yi mamu laifi. kada ka kai mu wurin jaraba, amma ka cece mu daga mugu. Amin.

## Agaishe ki Maria

Agaishe ki Maria, ke da ki ke cike da gracia. Ubangiji yana tare da ke, mai albarka kike a cikin mata, mai albarka ne kuma dan cikin ki Yesu. ya maria mai Tsarki, uwar Allah, ki roko mamu masu zunubi, yanzu da lokacin mutuwarmu. Amin.

## Daukaka ga Uba

Daukaka ga Uba, da Da, da Ruhu mai Tsarki. kamar yadda ake yin sa tun a farko, a yanzu, da har abada. Daga sara zuwa sara. Amin.

## Ya Yesu

Ya Yesu. ka gafarta mamu zunubain mu, ka cece mu daga wutan jahanama. ka kai duka rayuka cikin samaniya masaman wandada ke niman gafartawa. kadda ka kai mu cikin jaraba amma ka cece mu daga dukan mugunta. Amin.

## Ageishe ki Sarauniya mai Tsarki

Ageishe ki Sarauniya mai Tsarki, maman jinkai, mun mika maki rai mu, da dadin mu, da kuma fatan mu. A gare ki muke kuka, yaran hawawu da aka tawaye. A gare ki muke miko gunagunin mu, bakin ciki da hawaye a wannan inuwan hawaye. Juya idanun ki masun jinkai gare mu, budurwa Maria mai alheri, ku nuna mamu albarkacin Da cikin ki Yesu. Ya mai jinkai, ya mai kauna, ya budurwa Maria mai dadi. Amin

# ADDU'AR ROSARI TA YARA LABARU MASU FARIN

### 1. Shelar haifuwar Yesu - Mariya ta yi ciki ta ikon Ruhu Mai Tsarki

An aike mala'ika Jibrilu zuwa wajen Mariya a kasar Nazarat, ya zo ya tambaye ta ko za ta amince ta zama Uwar Yesu? Ya fada mata cewa, "Allah ne da kansa zai zama Ubansa." Domin Mariya ta gaskata cewa Allah zai iya aikata komai, sai ta ce, "I." Ya Mariya Uwar Allah, muna rokonki, ki bamu bangaskiya irin taki domin a kullayaumi mu koya daga gare ki yadda za mu saurare Allah, mu kuma aikata duk abin da ya umurce mu mu yi a cikin bangaskiya..

### 2. Ziyarar Mariya - Mariya dauke da jaririn cikinta-Yesu-, ta ziyarci 'yar uwarta Alisabatu.

Mala'ikan Allah ya fada wa Mariya cewa, " 'Yar uwarta Alisabatu ma tana da ciki." Nan take sai Mariya ta tashi da hanzari ta je domin ta taimake ta. A sa'adda suke gaisuwa, sai Alisabatu ta ji yadda 'Dan cikinta ya yi motsi da karfi don murna. Ruhu Mai Tsarki ne ya haskaka ta domin ta fahimci wannan abin al'ajibin cewa, Mariya Uwar Allah ce. Sai Alisabatu ta daga murya da karfi ta ce, "Ke Mai Albarka ce Mariya, domin kin gaskata!" Ya Mariya Uwar Allah, muna addu'a ki yi roko domin dukan masu yada bishara wadanda suke kokarin kawo Allah kusa da mutane domin su sadu da zukata masu taushi wadanda suke shirye su yi na'am da karbar bisharar Yesu da farin ciki, su kuma gaskata da shi.

### 3. Haifuwar Yesu - Mariya ta haifi Yesu a Baitalami.

A sa'adda Yusufu da Mariya suka iso Baitalami, sai ya zama tilas ne su kwana a cikin garken dabbobi-nan fa aka haifi Yesu- domin babu dakin kwanciya dominsu a masaukin. Mutane na farko da suka zo suka gani, da kuma suka yi ma Yesu sujada makiyaya ne. Mala'iku ne suka bayyana musu cewa an haifi Mai Ceto wanda shi ne Almasihu. Ya Mariya Uwar Allah, muna addu'a ki roka domin dukan yara da iyalansu wadanda ba su da gidajen kwanciya, da wadanda suka rasa gidajensu a dalilin yake-yake da annoba. Ki aiko da mutane da za su lura da su, ki kuma ba su salamar Allah.

### 4. Mikawa a Haikali - Mariya ta kai Yesu cikin Haikali ta mika shi ga Allah.

Bayan kwanaki arba'in (40), Yusufu da Mariya suka dauki jaririn nan Yesu, suka tafi Haikali a Urushalima bisa ga umurnin shari'a ta Yahudawa. Suna cikin Haikalin, sai mai tsarkin nan dattijo kuma, mai suna Saminu, ya shigo cikin Haikalin. Ruhu Mai Tsarki tun can ya fada masa ko wanene 'dan Yaron nan. Cike da murna da bangirma, Saminu ya dauki Yesu a cikin hannuwarsa sai ya ce, " Yanzu idanuna sun ga ceton nan, da haske wanda yake bayyana wa dukan al'ummai." Ya Yesu, muna rokonka saboda dukan mutane wadanda har yanzu ba su sanka ba. Ka basu alheri da zarafi domin su ji sakonka da kuma su gane cewa , kai kadai ne Haske da Ceton duniya.

### 5. An sami Yesu a cikin Haikali.

A sa'adda Yesu yake shekaru 12, sai suka tafi Urushallima da iyayensa domin su yi sujada a Haikali a lokacin Idin Ketarewa. Bayan idin, Yesu ya dakata daga baya a cikin Haikalin, yana koyarwa ga malamai batun Mulkin Allah Ubansa. A cikin rashin sani, sai Mariya da Yusufu suka tafi gida suna tsammanin Yesu yana tare da su. Da suka iso gida, sai suka gane cewa ashe Yesu ba ya tare da su. Sai suka koma zuwa Urushalima cikin hanzari domin su nemo shi, har sai da suka same shi a cikin Haikalin. Ya Allah Uba, muna rokonka saboda dukan iyaye wadanda suka rasa 'ya'yansu, ko kuma suke cikin damuwa saboda 'ya'yansu, da kuma wadanda suke begen haifan 'ya'ya, amma sun damu kwarai saboda matsalolin yau da kullum. Ka taimake su su sa begensu a cikinka, su kuma sani cewa kana tare da su a cikin kowace irin hali da suka sami kansu.